## Faɗakarwa :

1. Ba a rama sallar khusufi idan ba a san da khusufin ba sai bayan tafiyarsa.

2. Sanin dalilin yin khusufi ta hanyar ilimin zamani baya kore cewa ayoyi ne daga cikin ayoyin Allah. Allah yana tsoratar da bayinsa da ita, saboda haka ya dace ga musulmi ya shagalta da bauta wa Allah da ƙasƙantar da kai zuwa gare shi, ba wai ya shagalta da bibiyar khusufin ba. An karɓo daga Abu Bakhrata – Allah ya yarda da shi – ya ce, «Rana ta kisfe a zamanin Manzon Allah (S.A.W) sai Manzon Allah (S.A.W) ya fito yana jan mayafinsa..» Wannan yana nuna tsananin tsoron Manzon Allah (S.A.W) ga khusufi.

3. Ana samun raka'a a sallar khusufi da riskar ruku'un farko, duk wanda ruku'un farko ya kubce masa, amma ya samu na biyu, to raka'ar ta wuce shi, sai ya ramata bayan liman ya yi sallama, kamar yadda aka yi ta.

4. Ana yin sallar khusufi a cikin lokutan da hana sallah.

5. Ba a shar'anta yin sallar khusufi ba, saboda samun labari kawai, har sai an gani ƙuru-ƙuru.

www.al-feqh.com/ha

